(Hausa) 101 مدنی پھول

# LU'A LU'AN MADINA 101



Shehun Darika Jagoran Ahlussunnah
Mahassasin Kungiyar Dawatul Islami Masani Maulana Abu Bilal
**MUHAMMAD ILYAS**
Attar Qadiri Razavi دامت برکاتہم العالیہ

Fassarar Hausa
Daga Shashen Fassara
Na Dawat-ul-Islam

101مَدَنی پُھول

## 101 Madani Phool

# LU'A LU'AN MADINA 101

Majlis Al-Madina-tul-Ilmiyya ya gabatar da wannan littafin da harshen Urdu. Wanda **Sashenan mai kula da fassara na Dawat-e-Islami** ya fassara shi izuwa harshen Hausa. Idan kun sami kuskure a cikin Fassarar ko abun da littafin ya kunsa, da fatan za a yi kokarin sanadda sashen fassara (department de traduction) a adresin na akwatin sakonni, lambar waya ko imel mai zuwa, don samun lada mai yawa.

**Département de traduction (Dawat-e-Islami)**

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah, Mahallah Saudagran, Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan

**UAN :** ☎ +92-21-111-25-26-92 – Poste. 7213

**E-mail:** french.translation@dawateislami.net

**Lu’a lu’an Madina 101**

Fassara Hausa ta « 101 Madani Phool »

✂

## DUKKAN HAƘƘOƘIN MALLAKA

Copyright © 2024 Maktaba-tul-Madinah

Ba a yarda ba sake buga wa ko watsa wani ɓangare na wannan ɗaba’ar ta kowace hanya, ko tsari ko ta wani ha’li, na lantarki, na’ura, kwafi, rikodi ko waninsa, ba tare da rubutaccen izinin Maktaba-tul-Madinah ba.

**1ère parution :** Jumādil Saani 1446, AH – (Dec 2024)

**Éditeur :** Maktaba-tul-Madinah

**Quantité :** -

**ISBN :** -

## DAUKAR NAUYI

Kada ku yi wata-wata, ku kira mu domin daukar nauyin buga wani littafi addini domin aika ladan ga mamacinku a cikin dangin ku.

**Maktaba-tul-Madinah**

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah Mahallah Saudagran,
Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan

✍**E-mail :** global@maktabatulmadinah.com | feedback@maktabatulmadinah.com

✆ **Téléphone :** +92-21-34921389-93

💻**Web:** www.dawateislami.net | www.maktabatulmadinah.com

اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ وَ الصَّلٰوةُ وَ السَّلَامُ عَلٰى خَاتَمِ النَّبِيّٖنَ

اَمَّا بَعْدُ فَاَعُوْذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيْطٰنِ الرَّجِيْمِ بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ

## Addu'ar karanta littafi

Ku karanta Addu'ar nan kahin fara karatun littafin addini ko kuma wani darasi na musulumci, za ku tuna duk abunda kuka karanta عَزَّوَجَلَّ اِنْ شَآءَاللّٰه :

اَللّٰهُمَّ افْتَحْ عَلَيْنَا حِكْمَتَكَ وَانْشُرْ
عَلَيْنَا رَحْمَتَكَ يَا ذَاالْجَلَالِ وَالْاِكْرَام

### FASSARA

Ya Allah عَزَّوَجَلَّ ! Ka buɗa mana kofofin sani da hikimar ka, ka lulluɓemu da rahamar ka, ya ma'abuci daukaka da girma ! *(Al-Mustatraf, vol. 1, p. 40)*

**Lura:** kuyi Salati ga Annabi ﷺ sau daya kafin a yi addu'a da bayan addu'ar.

# Abubuwan da littafin ya kunsa

LU'A LU'AN MADINA 101 ........ 1
Falala Salāti-ga-Annabi ﷺ ........ 1
Lu'a lu'an Madina 11 akan Sallāma ........ 2
Lu'a lu'an Madina 14 akan Musafaha ........ 5
Lu'a lu'an Madina 12 akan magana ........ 8
Lu'a lu'an Madina 17 akan atishawa ........ 10
Lu'a lu'an Madina 9 akan yankan farce ........ 14
Lu'a lu'an Madina 7 akan sanya takalma ........ 17
Lu'a lu'an Madina 12 akan shiga-da-fita daga gida ........ 19
Lu'a lu'an Madina 4 akan shafa khôlli ........ 23
Lu'a lu'an Madina 15 akan tashi da konciya ........ 25
Abinda ake nema a wajan Muballighīn da Muballighāt (wa'izai maza da mata) ........ 28
Madani Channel - Paramètres de couverture globale ........ 30

اَلۡحَمۡدُ لِلّٰهِ رَبِّ الۡعٰلَمِيۡنَ وَ الصَّلٰوةُ وَ السَّلَامُ عَلٰى خَاتَمِ النَّبِيّٖنَ

اَمَّا بَعۡدُ فَاَعُوۡذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيۡطٰنِ الرَّجِيۡمِ بِسۡمِ اللّٰهِ الرَّحۡمٰنِ الرَّحِيۡمِ

# LU'A LU'AN MADINA 101

Duk yunkurin shaiɗan na ganin sai ya hana ku karanta wanna littafin, اِنۡ شَآءَاللّٰه عَزَّوَجَلَّ to kuyi kokarin karantashi gaba ɗaya domin ku koyi sunnonin babban masoyin mu Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

## Falala Salāti-ga-Annabi ﷺ

Manzon Allah (tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) mafi karamci da kyautatawa kuma mafi so-yuwa a gremu (صَلَّى اللّٰهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم) ya ce : « Ranar kiyama babu wata inuwa face inuwar Al'arshin Allah عَزَّوَجَلَّ. [Nau'ikan mutane] uku ne za su kasance a karkashin wannar inuwar Al'arshen. » Sai aka tambaye sa (tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi) : « ya ma'aikin Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, suwa ne waɗannan ? » Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace : « wanda ya yayema al'ummata kunci ; wanda ya raya sunnata da kuma wanda yake yawaita muni salati. » *(Al-Budoor-us-Saafirah fi-Umoor-il-Aakhirah, shafi na 131, Hadīthi na 366).*

صَلُّوۡا عَلَى الۡحَبِيۡب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

Mazon rahama, mai ceton al'Umma, mai aljannah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya faɗa: « duk wanda yake son Sunnah ta, ya na so na duk wanda yake sona ya na tare ni a cikin Aljannah. » *(Mishkāt-ul-Masābīh, juz'i. 1, shafi na 55, Hadisi na 175)*.



www.dawateislami.net

*Seenah tayri Sunnat ka Madina banay Aaqā*
*Jannat may parausi mujhay tum apna banānā*

*Ina fatan zuciya ta ta zama Madina sunnar ka, ya kay masoyi na*
*A cikin Aljanna, ka bani wurin zama a kusa da kay.*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب      صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Lu'a lu'an Madina 11 akan Sallāma

1. Ya na daga Sunnaĥ lokacin da ka haɗu da musulmi, kayi masa sallama.

2. Ga wani ɗan taqaitaccen bayani daga shafi na 102, mujalladi 16 na Littafin Bahār-e-Shari'a, wanda Maktaba-tul-Madina ta dauki yaunin bugawa da yaɗawa: « Niyyar da zanyi a zuci wajen yin sallama ita ce, dukiya, da mutunci da daraja wanda nikema sallama suna karkashin kaariyata, kuma a gu na bai halalta ba [haramun ne] taba ɗay daga cikinsu. » *(Bahār-e-Sharī'at, Juz'i na 16, shāf na 102)*

3. Yana da falala yin sallama ga musulmay, koma sau nawa a duk inda aka haɗu a yinin, koda a shiga wani wage ne kuma a futo.

4. Sounnaĥ ce ka kasance na farko wanda zai fara yin sallama.

5. Wanda ya fara yin sallama, shine mafi kusanci ga Allah عَزَّوَجَلَّ.

6. Wanda ya fara yin sallama ya kuɓuta daga girman kay, kamar faɗa Annabin mu masoyi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيۡهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم : « Wanda ya fara yin sallama ya kuɓuta daga girman kay. » *(Shu'ab-ul-īmān, Juz'i na 6, shafi. 433)*.

7. Rahama tasa'in ke sabka ga wanda ya fara yin sallama sanan goma ga wanda ya mayar masa. *(Kīmiyā-e-Sa'ādat)*.

8. Ana samun lada 10 yayin da aka faɗi "اَلسَّلَامُ عَلَيۡكُم", lada 20 kari, idan ankara da "وَرَحۡمَةُ الله" sanan lada 30 in ankara da "وَبَرَكَاتُه". Wa ɗansu mutane suna karawa da "جَنَّتُ المقام" da دوزخُ الحرام wanda hakan ba daidai bane. Wa dansu mashirmata suna karawa da kalmomi kamar haka, diyanku bayin mune, مَعاذالله. A'lā Hadrat, Imam-e-Ahl-e-Sunnat, Maulana Shaikh Imam Ahmad Raza Khan رَحۡمَةُ اللّٰهِ عَلَيۡه ya faɗa a shafi na 409, mujalladi na 22 Fatāwā Razawiyyah : « ya wajaba akalla mu furta kalmomin nan "اَلسَّلَامُ عَلَيۡكُم", anso a kara da "وَرَحۡمَةُ الله", wanda yafi kuma shine a kara da "وَبَرَكَاتُه" sanna ba za akara komai daga sama. Shi kuma, mai amsawa zai maida akalla kalmomin da aka yimasa sallama, amma fa anhi so yakara cikin amsa. Misali, idan ance masa "اَلسَّلَامُ عَلَيۡكُم", to shi kuma zai maida da "وَعَلَيۡكُمُ السَّلَامُ وَرَحۡمَةُ الله". Idan ko akace masa "اَلسَّلَامُ عَلَيۡكُم وَرَحۡمَةُ الله", to shi kuma zai maida ne da "وَعَلَيۡكُمُ السَّلَامُ وَرَحۡمَةُ الله وَ بَرَكَاتُه". Idan mai sallam ya furta ha'izuwa "وَبَرَكَاتُه", to mai amsawa ba zai kara komai daga hakanan. واللهُ تعالىٰ أعلم

9. Kamar yanda a wajan sallama ake samun lada 30 haka nan ake samun idan aka amsa da "وَعَلَيۡكُمُ السَّلَامُ وَرَحۡمَةُ الله وَبَرَكَاتُه".

10. Wajibi ne amsa sallama (da zarin anyi maka sallama) da

murya da zata jiyarda wanda yayi maka sallama.

11. A koyi yanda ake furta sallama daidai da kuma yadda ake mayar da sallama. Da farko, zan faɗa ; say ku maimaita baya na "اَلسَّلَامُ عَلَيْكُمْ (اَس۔سَلَامُ۔عَلَیۡ۔کُمۡ)", yanzu kuma zan faɗi amsa say ku maimaita bayan ni kamar haka "وَعَلَيْكُمُ السَّلَام (وَعَلَیۡکُ۔مُس۔سَلَام)".

Domin koyon sunnoni akan dubban batutuwa daban-daban, ku saye kuma ku karanta littatafan nan « Bahār-e-Sharī'at » Mujalladi 16, littafi mai shafi 312, da kuma « Sunnatayn aur Aadaab », littafi mai shafi 120, wanda Maktaba-tul-Madina ta tallata. Ɗay daga hanyoyi mafifita da za akoyi sunnoni itace tafiya cikin tawagar "Madani Qāfilahs" ta Dawat-e-Islami tare da masoyen Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

*Seekhnay Sunnatayn Qāfilay mayn chalo*
*Lootnay rahmatayn Qāfilay mayn chalo*

*Haun gi hal mushkilayn Qāfilay mayn chalo*
*Pao gey barakatayn Qāfilay mayn chalo*

*Domin koyon Sunna, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*
*Domin samun tagomashi, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*

*Domin magance matsalolinku, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*
*Domin samun albarka, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب　　صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

Yan uwa a musulunci! a karshe, ku bari in yi anfani da wannan dama don fitar da fifikon Sunnah ta hanyar hadisai da

kyawawan halaye. Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace: « duk wanda yake son Sunnah ta, ya na so na duk wanda yake sona ya na tare ni a cikin Aljannah. » *(Mishkāt-ul-Masābīh, Juz'i na 1, shafi na 55, Hadisi na 175)*.

*Seenah tayri Sunnat ka Madina banay Aaqā*
*Jannat may parausi mujhay tum apna banānā*

*Ina fatan zuciya ta ta zama Madina sunnar ka, ya kay masoyi na*
*A cikin Aljanna, ka bani wurin zama a kusa da kay.*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Lu'a lu'an Madina 14 akan Musafaha

1. Lokacin da musulmai biyu suka haɗu, yana daga sunna suyi musafaha (suba junan su hannu bayan sallama.

2. Kuyima junan ku sallama lokacin da zaku tafi, kuma kuna iya musafaha.

3. Wata faɗa [ hadithi ] ta masoyin mu Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم: « Yayin da musulumi suka ninka hannayen su lokacin haɗuwarsu, Allah عَزَّوَجَلَّ yana saɓko da rahama dari a tsakanin su, daga ciki tasa'in da tara ga wanda ya haɗu da ɗan uwansa da farin ciki kuma yake tambaya akan halin dan uwansa ta hayya mafi kyau. » *(Al-Mu'jam-ul-Awsat, Juz'I na 5, shafi na 380, lamba 7672)*.

4. Lokancinda aboki da abokinsa suka haɗu, suka yi musafa suka yi salati ga Annabi mai girma صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم, zunubban su da sukayi a baya da nan gaba kahin su rabu



www.dawateislami.net

an gāfarta musu. *(Shu'ab-ul- īmān lil-Bayhaqī, juz'I na 6, shafi na 471, Hadisi na 8944).*

5. Idan da iko, tun kahin su saki hannayensu suna iya yin wanna addu'a bayan Salāti ga Annabi: "يَغْفِرُ اللهُ لَنَا وَلَكُمْ" Allah عَزَّوَجَلَّ ya gafarata muna mu da ku.

6. Addu'a da musulmi biyu sukeyi yayin musafaha اِنْ شَآءَاللّٰه karɓaɓɓiya ce kuma su biyun za a gafarata musu kahin su saki hannayen su, اِنْ شَآءَاللّٰه. *(Musnad Imam Ahmad Bin Hanbal, juz'I na 4, shafi na 286, Hadisi na 12454)*

7. Musafaha (Sāda hannu da hannu) na kore rashin jituwa.

8. Masoyin mu Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya faɗa « musulmin da ya gaisa da hannunsa da ɗan uwansa alhāli babu kiyayya cikin zuciya ɗayan su, Allah عَزَّوَجَلَّ zai gafarta musu zunubbansu da nabaya ka hin hannayensu su rabu, kuma duk wanda ya kalli dan uwansa kallon na so ba tare da kiyayya ba a zuciya shi, to zunubbansu su biyun za a gafartamusu kahin su kauda ka wunan su. » *(Kanz-ul-'Ummāl, juz'i na 9, shafi na 57)*

9. Kuna iya gaisawa da hannayanku a dukan haduwarku.

10. Ba ya daga sunnaĥ ga masu gaisawa su biyun anfani da hannu guda wajan gaisuwa. Abunda ke sunna shine anfani da hannaye guda biyu wajan gaissawa.

11. Wadansu mutane basu haɗa hannayen saidai kawai su shafa yatsotsin su; wannan kuma baya daga Sounnaĥ.

12. An karhanta mutum ya sumbanci hannusa dakansa bayan gaisuwa, yen uwa musulmai masu wanna tabi'ar sumbantar hannayen su ya wajaba su rabu da wanna tabi'a. *(Bahār-e-Sharī'at, juz'i na 16, shafi na 115)*

13. Idan ana jin sha'awa yayin haɗa hannumu da ''Amrad'' (yaro mai kweu najan hankali) to ya haramta gaisawa ta hannu dashi. Kallonsa ma kaway zunubi ne idan yana tayar da sha'awa inda angansa. *(Durr-e-Mukhtār, juz'i na 2, shafi na 98)*.

14. Ita sunnah dai ta musafaha, dole sai ya zamanto ba komai a hannayen wanda zai hana saduwar su ba, bai dace rike wani abu yayin musafaha, kamar kelle. *(Bahār-e-Sharī'at, juz'i na 16, shafi na 98)*.

Domin koyon sunnoni akan dubban batutuwa daban-daban, ku saye kuma ku karanta littatafan nan « Bahār-e-Sharī'at » Mujalladi 16, littafi mai shafi 312, da kuma « Sunnatayn aur Aadaab », littafi mai shafi 120, wanda Maktaba-tul-Madina ta tallata. Ɗay daga hanyoyi mafifita da za akoyi sunnoni itace tafiya cikin tawagar ''Madani Qāfilahs'' ta Dawat-e-Islami tare da masoyen Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

Yan uwa a musulunci! a karshe, ku bari in yi anfani da wannan dama don fitar da fifikon Sunnah ta hanyar hadisai da kyawawan halaye. Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace: « duk wanda yake son Sunnah ta, ya na so na duk wanda yake sona ya na tare ni a cikin Aljannah. » *(Mishkāt-ul-Masābīh, vol. 1, p. 55, Hadisi na 175)*.



www.dawateislami.net

## Lu’a lu’an Madina 12 akan magana

1. Ku tattauna cikin fara'a da murmushi.

2. Tare da niyyar faranta wa musulmai rai, ku aje muryar ku kasa mutuntawa ga manya da abokantaka yara. اِنْ شَآءَاللّٰہ, banda ma samun lada, za ku riƙi matsayi na girmamawa a gaban su.

3. Ba ya daga sunnah, ɗaga murya kamar kuna ihu, yadda abokai da yawa suke yi idan suna magana a tsakanin su a wannan zamani na mu.

4. Tare da niyyoyi masu kyau, kurinka zancen da ladabi ga manya, har ma jariri. Ɗabi'un ku za su inganta kuma yaron zai koyi girmamawa yayin zance.

5. Kada mutum ya dinga yin wani abu da wasu ke ganin yana da banƙyama, kamar taɓa al'aura, cire datti daga jiki da yatsu, taba hanci, ko sanya yatsu a cikin kunnuwa ko hanci, ko tofi akai-akai. Mutane suna cutuwa da irin waɗannan ayyukan.

6. Ci gaba da sauraron mutumin cikin nutsuwa muddin yana magana. Fara fadin abin da kuke so ku ce ta hanyar katse shi ba Sunna ba ne.

7. Kuma a kowane hali, kada ku kya-kyacewa da dariya, domin Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم bai taɓa yin dariya ba.

8. Yawan magana da dariya akai-akai suna zubar da mutuncin mutum.

9. Yawan magana da dariya suna zubar da mutuncin mutum. Manzon rahama صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya ce: « Idan kuka ga wanda Allah ya albarkace shi da ƙin duniya da (sifa) mai magana kaɗan, to ku nemi kusanci da shi. hikima aka ba shi. » *(Sunan Ibn Mājah, juz’i na 4, shafi na 422, Hadisi na 4101)*.

10. Annabi masoyin mu صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya ce : « Wanda ya lazumci shiru yana samun amunci. » *(Sunan-ut-Tirmiẓī, juz’i. 4, shafi na 225, Hadisi na 2509).*

Yazo cikin Mir'āt-ul-Manājīh na Hujjat-ul-Islam, Sayyiduna Imam Muhammad Bin Muhammad Ghazāli عَلَيْهِ رَحْمَةُ اللّٰهِ الْوَالِى ya ce : « Akwai nau'ikan tattaunawa guda huɗu : (1) Gaba daya mai cutarwa, (2) Mai fa'ida gaba daya, (3) mai fa'ida da cutarwa kuma, (4) ta karshe wanda ba ta cutarwa kuma ba tada fa’ida. Yakamata a guji tattaunawa mai cutarwa gaba daya ; kuma dole ne yin tattaunawa wanda ke da fa'ida gaba ɗaya. Dangane da zance mai fa'ida kuma mai cutarwa, sai a kiyaye domin ya fi kyau kada a yi irin wannan hirar. A ƙarshe, nau'in zance na huɗu ɓata lokaci ne. Yana da wuya a bambance waɗannan nau'ikan tattaunawa, don haka shiru ya fi kyau. » *(Mir'āt-ul-Manājīh, juz’i na 6, shafi na 464)*

11. Lokacin da kuke magana da wani, dole ne ku kasance da kyakkyawar manufa a bayan jawabinku. Kuyi magana koyaushe da mutane bisa iya jurewarsu da hankullan su (fahimtar su).

12. Ku guji amfani da muggan kalamai ko batsa. A dena zagi. Kar a manta! Rantsuwa ga musulmi ba tare da izinin addini ba (Shar'ī) haramun ne kwata-kwata. *(Fatāwā Razawiyyah, juz’i. 21, shafi na 127)*, kuma Aljanna haramun ce



www.dawateislami.net

ga wanda ya yi amfani da kalaman ɓatanci ko batsa. Manzon صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya ce: « Aljanna ta kasance haramun ga wanda ya yi kalaman ɓatanci. » *(Kitāb-us-Samt ma'a Mawsu'ah, juz'i na 7, shafi 204, Lamba 325).*

Domin koyon sunnoni akan dubban batutuwa daban-daban, ku saye kuma ku karanta littatafan nan « Bahār-e-Sharī'at » Mujalladi 16, littafi mai shafi 312, da kuma « Sunnatayn aur Aadaab », littafi mai shafi 120, wanda Maktaba-tul-Madina ta tallata. Ɗay daga hanyoyi mafifita da za akoyi sunnoni itace tafiya cikin tawagar ''Madani Qāfilahs'' ta Dawat-e-Islami tare da masoyen Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب          صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

Yan uwa a musulunci! a karshe, ku bari in yi anfani da wannan dama don fitar da fifikon Sunnah ta hanyar hadisai da kyawawan halaye. Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace: « duk wanda yake son Sunnah ta, ya na so na duk wanda yake sona ya na tare ni a cikin Aljannah. » *(Mishkāt-ul-Masābīh, juz'i na 1, shafi na 55, Hadisi na 175)*.

## Lu'a lu'an Madina 17 akan atishawa

kalmomi guda biyu masu albarka na Manzon صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم:

1. « Allah عَزَّوَجَلَّ yana son atishawa amma ba ya son hamma». *(Sahīh Bukhārī, juz'i na 4, shafi na 163, Hadisi na 6226).*
2. « Idan wani ya yi atishawa ya ce: "اَلْحَمْدُلِلّٰه", Mala'iku suna cewa "رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ", idan kuma ya ce: "رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ", sai Mala'iku su

ce « Allah عَزَّوَجَلَّ ya muka rahama. » *(Al-Mu'jam-ul-Kabeer, juz'i na 11, shafi na 358, Hadisi na 12284).*

3. Ka dukar da kan ka, ka rufe fuskarka idan za ka yi atishawa, sannan ka yi atishawa da murya kasa-kasa domin wauta ce yin atishawa da karfi. *(Radd-ul-Muhtār, juz'i na 9, shafi na 684).*

4. Ya wajaba a ce "اَلْحَمْدُ لِلّٰه" bayan yin atishawa. (Ya zo a cikin Khazā`in-ul-'Irfān a shafi na 3 dangane da Tahtaawī cewa Sunnah ce mai karfi yin godiya ga Allah عَزَّوَجَلَّ bayan atishawa). Zai fi kyau a ce "اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْن" ko kuma "اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ عَلٰى كُلِّ حَال".

5. Wājibi ne fadar "يَرْحَمُكَ الله" (Allah عَزَّوَجَلَّ ya muka rahama) ga wanda yayi atishawa, ba tare da wata-wata ba kuma da muryar da za ta jiyar dashi. *(Bahār-e-Sharī'at, juz'i na 16, shafi na 119).*

6. Indan yaji an ce masa "يَرْحَمُكَ الله", mutumin da yayi atishawa zai ce : "يَغْفِرُ اللهُ لَنَا وَ لَكُمْ" (Allah عَزَّوَجَلَّ ya muna gafara da mu da ku) ko ya ce : "يَهْدِيْكُمُ اللهُ وَ يُصْلِحُ بَالَكُمْ" (Allah عَزَّوَجَلَّ ya shiryeku kuma ya yaye damuwar ku). *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na 5, shafi na 326).*

7. Wanda ko yace اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ عَلٰى كُلِّ حَال bayan atishawa, sai yabi da harshen sa akan hakoran sa gaba ɗay, zai zama kariya a gareshi daga cututtuka na haure, اِنْ شَآءَ الله. *(Mir'āt-ul-Manājīh, juz'i na 6, shafi na 396).*

8. Chugaban mu Ali رَضِىَ اللّٰهُ عَنْهُ ya faɗa cewa : « Duk wanda ke faɗar "اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ عَلٰى كُلِّ حَال" lokacin da yayi atishawa, ba zai ta ɓa ciwon haure ko na kunne ba. » *(Mirqāt-ul-Mafātīh, juz'i na 8, shafi na 499, Taht ul-Hadīth 4739).*



www.dawateislami.net

9. Wanda ya yi atishawa ya wajaba ya faɗi "اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ" da murya me jiyarwa, domin a jishi kuma a amsa masa. *(Radd-ul-Muhtār, juz'i na 9, shafi na 684).*

10. Amsar [wato : "يَرْحَمُكَ الله"] Wājib ne a farkon atishawa, shima sai idan mai atishawa yace "اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ" amma idan yayi atishawa ta biyu anan an so a mayar masa, ba Wajibi ne ba Mustahabbi ne). *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na 5, shafi na 326)*.

11. Amsa Wājib ne kawai idan mai atishawa ya ce "اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ", idan bai faɗa ba babu amsa. *(Bahār-e-Sharī'at, juz'i na 16, shafi na 120)*

12. Idan wani yayi atishawa yayin da liman ke hutuba, to wanda ya jishi ba zai amsa masa ba. *(Fatāwā Qādi Khān, juz'i na 2, shafi na 377)*

13. Idan 'yan'uwa Musulmi da yawa suka taru kuma a ka samu wasu sun ba da amsa, amsar za tazama a madadin kowa, amma yana da kyau kowa ya amsa. *(Radd-ul-Muhtār, juz'i na 9, shafi na 684)*

14. Idan wani ya yi atishawa daga dayan bangon sai ya ce : "اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ" to wanda ya ji sai ya amsa. *(Radd-ul-Muhtār, juz'i na 9, shafi na 684)*

15. Duk wanda ya yi atishawa a cikin Sallah, to ya yi shiru ; amma idan ya ce : "اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ", ba zai taɓa Sallah ba. Idan kuma ya yi shiru a lokacin Sallah, yana iya faɗar alhamdu'lillahi bayan ya gama Sallah. *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na 1, shafi na 98)*



www.dawateislami.net

16. Idan kana yin Sallah wani ya yi atishawa ka ce masa: "اَلْحَمْدُ لِلّٰہِ" da nufin ka amsa masa, sallarka ta ɓaci. *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na 1, shafi na 98)*

17. Idan kāfiri ya ce "اَلْحَمْدُ لِلّٰہِ" yayin da yake atishawa, sai a amsa masa da "يَهْدِيْكَ الله" (wato Allah عَزَّوَجَلَّ ya shiryar da kai). *(Radd-ul-Muhtār, juz'i na 9, shafi na 684)*

Domin koyon sunnoni akan dubban batutuwa daban-daban, ku saye kuma ku karanta littatafan nan « Bahār-e-Sharī'at » Mujalladi 16, littafi mai shafi 312, da kuma « Sunnatayn aur Aadaab », littafi mai shafi 120, wanda Maktaba-tul-Madina ta tallata. Ɗay daga hanyoyi mafifita da za akoyi sunnoni itace tafiya cikin tawagar "Madani Qāfilahs" ta Dawat-e-Islami tare da masoyen Annabi صَلَّی اللّٰہُ عَلَیْہِ وَاٰلِہٖ وَسَلَّم.

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

Yan uwa a musulunci! a karshe, ku bari in yi anfani da wannan dama don fitar da fifikon Sunnah ta hanyar hadisai da kyawawan halaye. Manzon Allah صَلَّی اللّٰہُ عَلَیْہِ وَاٰلِہٖ وَسَلَّم yace: « duk wanda yake son Sunnah ta, ya na so na duk wanda yake sona ya na tare ni a cikin Aljannah. » *(Mishkāt-ul-Masābīh, juz'i na 1, shafi na 55, Hadisi na 175)*.

*Sunnatayn 'aam karayn, Deen ka ham kaam karayn*
*Nayk ho jāyain Musalman, Madinay walay.*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد



www.dawateislami.net

## Lu'a lu'an Madina 9 akan yankan farce

1. Yankan farce Mustahabbi ne [an fi so] yanke farce ranar Juma'a. Duk da haka, kada ku jira har zuwa Juma'a idan faratunan ku sun yi tsayi. *(Durr-e-Mukhtār, juz'i na 9, shafi na 668)*

Cikin Sadr-ush-Sharī'ah, Badr-ut-Tareeqah, Maulana Amjad 'Ali A'zami رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه ya ce « Wanda yake yanke farce ranar Juma'a Allah عَزَّوَجَلَّ zai kare shi daga bala'o'i har zuwa ranar Juma'a mai zuwa, da kuma ƙarin kwana uku bayan haka, wato kwana 10. A wata ruwaya kuma ta zo cewa duk wanda ya ke yanke farce ranar Juma'a, rahama ta zo masa, kuma zunuban sa za su tafi » *(Durr-e-Mukhtār, Radd-ul-Muhtār, juz'i na 9, shafi na 668; Bahār-e-Sharī'at, juz'i na 16, shafi na 225-226)*.

2. Wanan mai zuwa shine taƙaitaccen hanyar da aka tsara don yanke farce: Fara da yatsa manuniyar hannun dama, sannan ku yanke sauran yatsun a jere har zuwa karamin ɗan yatsa, amma kada ku yanke farcen babban ɗan yatsa. Sannan, ku fara da yanke farce karamin ɗan yatsa hannun hagu, a jere a haɗa da babban yatsan hannun. A ƙarshe, sai a yanke babban ɗan yatsa na hannu dama. *(Durr-e-Mukhtār, juz'i na 9, shafi na 670; Ihyā-ul-'Uloom, juz'i na 1, shafi na 193)*.

3. Ba a ruwaito takamaiman tsari na yanke farcen ƙafa ba. Zai fi kyau a fara da ƙaramin yatsan ƙafar dama kuma a yanke a jere har da babban yatsan ƙafar, sannan a yanke farcen ƙafar hagu a jere daga babban yatsan zuwa ɗan yatsa karami. *(Durr-e-Mukhtār, shafi na 670)*.



www.dawateislami.net

4. Makruhi [abin kyama] ne yanke farce a halin Janaba, watau lokacin da Wanka yake farilla a kan mutum. *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na 5, shafi na 358)*.

5. Makruhi [abin kyama] ne mutum ya cire farce da hakora; akwai tsoron kamuwa da cutar kuturta ta yin hakan. *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na 5, shafi na 358)*.

6. Bayan an yake farce ya wajaba a bunne su, amma ba komai idan an jefar. (Ibid)

7. Makruhi [abin kyama] ne jefa farce a bayan gida ko banɗaki saboda yana haifar da rashin lafiya. *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na 5, shafi na 358)*.

8. Kada ku yanke farce a ranar Laraba domin yana iya haifar da cutar kuturta. Amma idan wani bai yanke farce ba har tsawon kwanaki 39, Laraba kuma ita ce kwana 40, (wato idan bai yanke farce ba a wannan ranar, zai wuce kwanaki 40), Wājib [wajibi ne] a kansa ya yanke farcen sa a wannan ranar (Laraba) saboda haramun ne kuma Makruh na Haramci a ki yanke farce sama da kwana arba'in. *(Domin samun cikaken bayani, zaku iya karanta daga shafi 574 zuwa 685 na Fatāwā Razawiyyah, juz'i na 22)*.

9. Dogayen faratuna wuri ne na Shaidan, wato Shaidan yana zaune a kan dogayen faratuna. *(Ithāf-us-Sādah liz-Zabeedī, juz'i na 2, shafi na 653)*

Domin koyon sunnoni akan dubban batutuwa daban-daban, ku saye kuma ku karanta littatafan nan « Bahār-e-Sharī'at » Mujalladi 16, littafi mai shafi 312, da kuma « Sunnatayn aur



www.dawateislami.net

Aadaab », littafi mai shafi 120, wanda Maktaba-tul-Madina ta tallata. Ɗay daga hanyoyi mafifita da za akoyi sunnoni itace tafiya cikin tawagar ''Madani Qāfilahs'' ta Dawat-e-Islami tare da masoyen Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

*Seekhnay Sunnatayn Qāfilay mayn chalo*
*Lootnay rahmatayn Qāfilay mayn chalo*
*Haun gi hal mushkilayn Qāfilay mayn chalo*
*Pao gey barakatayn Qāfilay mayn chalo*

*Domin koyon Sunna, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*
*Domin samun tagomashi, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*
*Domin magance matsalolinku, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*
*Domin samun albarka, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

Yan uwa a musulunci! a karshe, ku bari in yi anfani da wannan dama don fitar da fifikon Sunnah ta hanyar hadisai da kyawawan halaye. Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace: « duk wanda yake son Sunnah ta, ya na so na duk wanda yake sona ya na tare ni a cikin Aljannah. » *(Mishkāt-ul-Masābīh, vol. 1, p. 55, Hadīth 175)*.

*Sunnatayn 'aam karayn, Deen ka ham kaam karayn*
*Nayk ho jāyain Musalman, Madinay walay.*

*Puissions-nous répandre la Sounnaĥ et faire le travail du Deen.*
*Ô roi de Madina, que les musulmans deviennent tous pieux*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد



www.dawateislami.net

## Lu'a lu'an Madina 7 akan sanya takalma

1. Annabi masoyinmu صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yana cewa: « Ku yawaita amfani da takalmi, domin idan mutum ya sanya takalmi, kamar kana bias abin hawa (wato su na rage gajiya) matuqar ka sanya takalmi. » *(Sahīh Muslim, shafi na 1161, Hadisi na 2096)*.
2. Ku karkaɓe takalmanku kafin ku sanya, domin koda da kwori ko yan duwarwatsu a ciki za su fita.
3. Ku sanya takalmin kafar dama da farko, sannan hagu. Wajan cire su, cire hagu da farko sannan dama. Annabi masoyin mu صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya ce : « Duk wanda zai sanya takalmi daga cikinku, to ya fara da na kafar dama ; Sa'ad da zai cire su, sai ya fara da hagu, domin kafar dama ta kasance ita ce ta farko wajan sa wa, ta ƙarshe kuma wajan cire wa. » *(Sahīh Bukhārī, juz'i na 4, shafi na 65, Hadisi na 5855)*.

Ya zo a cikin Nuzhat-ul-Qaarī cewa: Idan za a shiga masallaci, a shiga da qafar dama, idan za a tashi, a fita da qafar hagu. Yana da wuya a yi aiki da waɗannan hadisan da muka ambata yayin shiga Masallaci. A'lā Hadrat, Imam Ahmad Raza Khan r ya samar da mafita a nan kamar haka: "Idan za ku shiga Masallaci, ku fudda takalmin hagu, ku sanya ƙafar hagu a kansa, sannan ku cire takalmin dama, ku shiga. Masallaci da ita. Idan za ku fita daga Masallaci, sai ku fitar da kafar hagu daga kofa, sannan ku dora a saman takalminku, sannan ku fitar da kafar dama, sannan ku sanya takalminku na dama sannan ku sanya takalmi na hagu. » *(Nuzhat-ul-Qaarī, juz'i. na 5 shafi na 530)*.



www.dawateislami.net

4. Maza su sanya takalman maza, mata su sanya takalma na mata.

5. Wani ya ce wa Sayyidatuna A'ishah رَضِیَ اللّٰہُ عَنْہَا cewa akwai macen da take sanya takalman maza. Sai ta amsa da cewa Manzon Allah صَلَّی اللّٰہُ عَلَیۡہِ وَاٰلِہٖ وَسَلَّم ya tsine wa macen da take qoqarin zama kamar maza. *(Sunan Abī Dāwood, p. 84, juz'I na 4, Hadisi na 4099)*

Sadr-ush-Sharī'ah, Badr-ut-Tareeqah, 'Allāmah Maulana Mufti Muhammad Amjad 'Ali A'zami رَحۡمَۃُ اللّٰہِ عَلَیۡہِ ya faɗa cewa : « bai halalta ba ga mata sanya takalman maza. Bugu da ƙari kuma, duk wani abu da ya bambanta jinsin biyu an hana su kwafin kishiyar jinsin, kada maza su duki salon mata, haka ma mata su dinga yin salon maza. *(Bahār-e-Sharī'at, juz'i na 16, shafi na 65)*.

6. Lokacin da kuke zaune, ku cire takalmanku, saboda wannan yana futar da ƙafafu.

Ɗaya daga cikin abubuwan da ke haifar da zullumi shine ganin takalma a jirkice kuma a bar shi a haka. Ya zo a cikin Dawlat-e-Be-Zawaal cewa: « Idan takalmi ya kasance juye a cikin dare, sai Shaidan ya zo ya zauna a kai, domin shi ne Al'arshinsa. » *(Sounnî Bahishtī Zaywar, juz'i. na 5 shafi na 604)*. Idan kuka ga wani takalmi da aka yi amfani da shi a jirkice, sai ku juya shi domin ya dawo daidai sa.

Domin koyon sunnoni akan dubban batutuwa daban-daban, ku saye kuma ku karanta littatafan nan « Bahār-e-Sharī'at » Mujalladi 16, littafi mai shafi 312, da kuma « Sunnatayn aur Aadaab », littafi mai shafi 120, wanda Maktaba-tul-Madina ta

tallata. Ɗay daga hanyoyi mafifita da za akoyi sunnoni itace tafiya cikin tawagar ''Madani Qāfilahs'' ta Dawat-e-Islami tare da mabiyan kuma masoyen Annabi صَلَّی اللّٰہُ عَلَیۡہِ وَاٰلِہٖ وَسَلَّم.

صَلُّوۡا عَلَی الۡحَبِیۡب صَلَّی اللّٰہُ عَلٰی مُحَمَّد

Yan uwa a musulunci! a karshe, ku bari in yi anfani da wannan dama don fitar da fifikon Sunnah ta hanyar hadisai da kyawawan halaye. Manzon Allah صَلَّی اللّٰہُ عَلَیۡہِ وَاٰلِہٖ وَسَلَّم yace: « duk wanda yake son Sunnah ta, ya na so na duk wanda yake sona ya na tare ni a cikin Aljannah. » *(Mishkāt-ul-Masābīh, juz'i na 1, shafi na 55, Hadisi na 175)*.

*Seenah tayri Sunnat ka Madina banay Aaqā*
*Jannat may parausi mujhay tum apna banana*

*Ina fatan zuciya ta ta zama Madina sunnar ka, ya kay masoyi na*
*A cikin Aljanna, ka bani wurin zama a kusa da kay.*

صَلُّوۡا عَلَی الۡحَبِیۡب صَلَّی اللّٰہُ عَلٰی مُحَمَّد

## Lu'a lu'an Madina 12 akan shiga-da-fita daga gida

1. Idan zaku fita daga gida, Sai Ku Karanta Wannan Addu'ar:

"بِسۡمِ اللّٰہِ تَوَکَّلۡتُ عَلَی اللّٰہِ لَاحَوۡلَ وَلَا قُوَّۃَ اِلَّا بِاللّٰہِ"

Da sunan Allah عَزَّوَجَلَّ, ina mai dogaro da Allah عَزَّوَجَلَّ, ba bu karfi da dubara sai wurin Allah عَزَّوَجَلَّ. *(Sunan Abī Dāwood, juz'I na 4, shafi na 420, Hadisi na 5095)*

اِنۡ شَآءَاللّٰہ da albarkar karatun wanna Addu'a, za ku kasance bisa



www.dawateislami.net

madai-daiciyar hanya, za a kare ku daga bala'o'i kuma za ku samu taimakon daga Allah عَزَّوَجَلَّ.

2. Addu'ar shiga gida ita ce :

"اَللّٰهُمَّ اِنِّيْٓ اَسْئَلُكَ خَيْرَ الْمَوْلَجِ وَخَيْرَ الْمَخْرَجِ بِسْمِ اللهِ وَلَجْنَا وَبِسْمِ اللهِ خَرَجْنَا وَعَلَى اللهِ رَبِّنَا تَوَكَّلْنَا۔"

*Ya Allah عَزَّوَجَلَّ, ina rokon ka alkhairin shiga da fita, muna shiga (gida) da sunan Allah عَزَّوَجَلَّ kuma muna fita (gida) da sunnan Allah عَزَّوَجَلَّ, kuma ga Allah عَزَّوَجَلَّ muka dogara (Sunan Abī Dāwood, shafi na 420, juz'i na 4, Hadisi na 5096)*

Bayan kun gama karanta Addu'ar, sai ku yi Sallama ga iyallan ku, sai kuma ku gabatar da salatinku ga babban masoyi Annabi (صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم), sanan sai ku karanta Suratul-Ikhlās. Za ku samu arziki da wadata (ci da sha) kuma za ku tsira daga saɓa ni na gida, اِنْ شَآءَ اللّٰه.

3. Ku yi Sallāma ga Muhar-raminku da Muhar-ramiyar ku (misali mahaifiyarku, mahaifinku, yayyeninku maza da mata, ƴaƴanku da matanku, da sauransu), lokacin shiga da fita daga gidanku.

4. Lokacin da wani ya shiga gida ba tare da ya ambaci sunan Allah عَزَّوَجَلَّ, misali ba tare da ya ce "بِسْمِ الله" Shaidan yana shiga da tare da shi.

5. Idan za ku shiga gidan da ba kowa (ko da gidankune), sai kuce:

"اَلسَّلَامُ عَلَيْنَا وَعَلٰى عِبَادِ اللهِ الصّٰلِحِيْنَ"

*Amuncin Allah ya tabbata a gare mu da salihan bayin Allah.*

Mala'iku zasu amsa wannan Sallama. *(Radd-ul-Muhtār, juz'i na 9, shafi na 682)*

Ko kuma kuce:

"اَلسَّلَامُ عَلَيْكَ اَيُّهَا النَّبِىُّ"

*Ya kai Annabi* صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم*! Amuncin yatabbata agareka.*

Comme l'âme sacrée et bénie du Prophète Bien-aimé et béni صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم est présente dans les maisons des musulmans. kamar yadda ruhi mai tsarki kuma mai albarka na Masoyin mu Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya kasance a gidajen musulmi. *(Bahār-e-Sharī'at, juz'i na 16, shafi na 96; Sharh-ush-Shifā lil-Qaarī, juz'i na 2, shafi na 118)*

6. Idan kana son shiga gidan wani, sai ka ce: « "اَلسَّلَامُ عَلَيْكُم" sai kace: in shigo? ».

7. Idan ba a ba da izinin shiga gidan ba, ku dawo da murna, watakila mazauna gidan sun ƙi saboda wani uziri (cilastawa).

8. Lokacin da wani ya buga ƙofar ku, Sunnaĥ shi ne ku tambaya: « Wane ne? » Sai wanda ya ƙwanƙwasa ya faɗi sunansa, misali « Muhammad Ilyās ». Ba Sunna ba ce « Madina ! », « Ni ne », « Bude kofa », da sauransu. Maimakon ya fadi sunansa.

9. Ka nisance kofa zuwa gefe guda bayan ka fadi sunanka, don kada idan an bude kofar gidan, ganinku yatafi kai tsaye a cikin gidan.

10. An haramta duba cikin gidan wani. A daura da gidajen wasu, wani lokacin akwai gidajen wasu a kan matakan wanda suke a kasa. Saboda haka, dole ne mutum ya kasance mai hankali lokacin neman daga baranda don tabbatar da cewa ba a duba cikin gidajensu ba.

11. Idan kun ziyarci wani, kada ku mu-zantar da tsarin gidansa, saboda yin haka zai iya cutar da shi.

12. Lokacin da zaku tafiyarku daga gidan 'yan uwa, ku gode musu, ku yi Sallama kuma ku yi qoqarin ba su wani ɗan littafi mai koyar da Sunna, da sauransu.

Domin koyon sunnoni akan dubban batutuwa daban-daban, ku saye kuma ku karanta littatafan nan « Bahār-e-Sharī'at » Mujalladi 16, littafi mai shafi 312, da kuma « Sunnatayn aur Aadaab », littafi mai shafi 120, wanda Maktaba-tul-Madina ta tallata. Ɗay daga hanyoyi mafifita da za akoyi sunnoni itace tafiya cikin tawagar "Madani Qāfilahs" ta Dawat-e-Islami tare da masoyen Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

*Seekhnay Sunnatayn Qāfilay mayn chalo*
*Lootnay rahmatayn Qāfilay mayn chalo*

*Haun gi hal mushkilayn Qāfilay mayn chalo*
*Pao gey barakatayn Qāfilay mayn chalo*

*Domin koyon Sunna, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*
*Domin samun tagomashi, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*

*Domin magance matsalolinku, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*
*Domin samun albarka, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللهُ عَلٰى مُحَمَّد

Yan uwa a musulunci! a karshe, ku bari in yi anfani da wannan dama don fitar da fifikon Sunnah ta hanyar hadisai da kyawawan halaye. Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace: « duk wanda yake son Sunnah ta, ya na so na duk wanda yake sona ya na tare ni a cikin Aljannah. » *(Mishkāt-ul-Masābīh, juz'i na 1, shafi na 55, Hadisi na 175)*.

*Seenah tayri Sunnat ka Madina banay Aaqā*
*Jannat may parausi mujhay tum apna banānā*

*Ina fatan zuciya ta ta zama Madina sunnar ka, ya kay masoyi na*
*A cikin Aljanna, ka bani wurin zama a kusa da kay.*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Lu'a lu'an Madina 4 akan Sanya kwalli

1. Cikin Sunan Ibn Mājah, akwai wata riwaya da ke cewa: « Mafi alherin kolli a duk cikin su shine Ismidi, domin yana inganta gani da kuma sanya gashin ido. » *(Sunan Ibn Mājah, juz'i na 4, shafi na 115, Hadisi na 3497)*

2. Hakanan ana iya amfani da Kohli da aka yi da duwatsu. Sai dai kuma abin kyama ne ga mutum ya yi amfani da bakin kolli da nufin yin ado, amma sai dai idan niyya ta kasance haka. *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na 5, shafi na 359)*.

3. Sunnaĥa ce amfani da kohli yayin barci. *(Mir'āt-ul-Manājīh, juz'i na 6, shafi na 180)*

4. Ga taqaitaccen hanyoyi guda uku da aka shar'anta yin amfani da kolli : (a) Wani lokaci ku shafa shi sau uku akan



www.dawateislami.net

kowane ido. (b) wani ɗan lokaci kuma sai a shafa a idon dama sau uku, sau biyu a idon hagu. (c) sauran lokutta, sai a shafa shi sau biyu a kowane ido, sannan daga karshe sai a dauko sandar, a saka a cikin kwandon yadda kolli din ya kwanta a kai, sai a yi amfani da wannan sanda sau daya a kowane ido *(Duba : Shu'ab-ul- īmān, juzu'i na 5, shafi. 218-219)* Idan an yin haka, za a aiwatar da hanyoyi guda uku da yarda Allah, اِنْ شَآءَاللّٰه.

Yan uwa musulmai ! Masoyin mu Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya kasance yana fara duk wani aykin alkhairi da dama, don haka kufar shafa kolli ga idon dama sanan idon hagu.

Domin koyon sunnoni akan dubban batutuwa daban-daban, ku saye kuma ku karanta littatafan nan « Bahār-e-Sharī'at » Mujalladi 16, littafi mai shafi 312, da kuma « Sunnatayn aur Aadaab », littafi mai shafi 120, wanda Maktaba-tul-Madina ta tallata. Ɗay daga hanyoyi mafifita da za akoyi sunnoni itace tafiya cikin tawagar "Madani Qāfilahs" ta Dawat-e-Islami tare da masoyen Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

Yan uwa a musulunci! a karshe, ku bari in yi anfani da wannan dama don fitar da fifikon Sunnah ta hanyar hadisai da kyawawan halaye. Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace: « duk wanda yake son Sunnah ta, ya na so na duk wanda yake sona ya na tare ni a cikin Aljannah. » *(Mishkāt-ul-Masābīh, juz'i na 1, shafi na 55, Hadisi na 175)*.

*Seenah tayri Sunnat ka Madina banay Aaqā*
*Jannat may parausi mujhay tum apna banānā*

*Ina fatan zuciya ta ta zama Madina sunnar ka, ya kay masoyi na*
*A cikin Aljanna, ka bani wurin zama a kusa da kay.*

صَلُّوْا عَلَى الْحَبِيْب        صَلَّى اللّٰهُ عَلٰى مُحَمَّد

## Lu'a lu'an Madina 15 akan tashi daga bacci

1. A kak-kaɓe gado da kyau kafin barci, domin idan da kwari masu guba, da dai sauransu. Za a fitar dasu.

2. Ku karanta wannan addu'ar kafin barci:

   اَللّٰهُمَّ بِاسْمِكَ اَمُوْتُ وَاَحْيَا

   Ya Allah عَزَّوَجَلَّ, da Sunanka nike mutuwa kuma ina rayuwa (ina barci kuma ina farkawa). *(Sahīh Bukhārī, juz'i na 4, shafi na 196, Hadisi na 6325)*

3. Kada ku yi barci bayan La'Asr, domin akwai tsoron rasa hankali. Annabi mai girma صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم ya ce : « Wanda yake yi barci bayan La'asar, kuma ya rasa hankali, to kada ya zargi kowa sai kansa kawai. » *(Musnad Abī Ya'lā, juz'i na 4, shafi na 678, Hadisi na 4897)*

4. Mustahabbi ne [an fi so] a yi barci na wani ɗan lokaci da rana. *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na 5, shafi na 376)*

   Cikin Sadr-ush-Sharī'ah, Badr-ut-Tareeqah, 'Allāmah Maulana Mufti Muhammad Amjad 'Ali A'zami رَحْمَةُ اللّٰهِ عَلَيْه yace : « Wanna zai yuyu ga wanda suke raya dare suna yin salla, da ambaton Allah, ko kuma suna karatu ko karanta litattafan addini, domin su kawar da gajiyar da ke tattare



www.dawateislami.net

dasu kasancewar su farke da daren ta hanyar barcin rana. »
*(Bahār-e-Sharī'at, juz'i na 16, shafi na 79)*

5. Makruhi [abin kyama] ne yin barci a farkon yini ko tsakanin Maghrib da isha'i. *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na 5, shafi na 376)*.

6. Barci cikin tsarki shine aka fi so.

7. Ku kwanta da farko gefenku na dama, kuna fuskantar alQibla, tare da hannun ku na dama kasan kumcin ku na dama, na wani ɗan lokaci, sanan saman hannunku na hagun a gefenku na hagun. *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na. 5, shafi na 376)*

8. Ku yi tunani game da kabari idan za ku yi barci, domin a cikin kabari za mu kaɗaita, kuma ba za a sami kowa ba tare da mu face ayyukanmu.

9. Idan za ku tayi barci, ku kula da ambaton Allah. Ku ci gaba da karanta Tahlil da Tasbīh da Tahmeed (wato ku ci gaba da karanta "لَآ اِلٰهَ اِلَّا اللهُ، سُبۡحٰنَ اللهِ، اَلۡحَمۡدُ لِلّٰهِ" har sai kun yi barci, domin fa mutum yana tashi cikin iri halin da ya konta, kuma a cikin ranar lahira, Mutum zai tashi a cikin irin halin da ya mutu a cikin shi.

10. Sai a karanta wannan addu'ar lokacin da aka farka:

"اَلۡحَمۡدُ لِلّٰهِ الَّذِیۡۤ اَحۡیَانَا بَعۡدَ مَاۤ اَمَاتَنَا وَاِلَیۡهِ النُّشُوۡرُ"

Dukkanin godiya da yabo su tabbata ga Allah عَزَّوَجَلَّ wanda ya raya mu bayan mun mutu kuma gareshine za mu komawa. *(Sahīh Bukhārī, juz'i na 4, shafi na 196, Hadisi na 6325)*

11. Ku ƙulla niyya tabbatacciya, idan kun tashi, ku riƙi taƙawa (tsoron Allah), kada ku jawo wa wasu wahala. *(Fatāwā 'Aalamgīrī, juz'i na 5, shafi na 376).*

12. Lokacin da yara maza da 'yan mata suka kai shekaru goma, a sanya su barci daban-daban. Ko yaro mai wannan shekarun bai kamata ya kwana da warinsa ko wanda suka girme shi a shekaru. *(Durr-e-Mukhtār, Radd-ul-Muhtār, juz'i na 9, shafi na 629)*.

13. Idan miji da mata suna kwana a kan gado ɗaya, kada su sa ɗan shekara goma ya kwana da su. Lokacin da yaro ya kai shekarun da zai iya jin sha'awa, dokokin maza za su hau akan shi. *(Durr-e-Mukhtār, juz'i na 9, shafi na 630)*

14. A dinga yin Assuwaki bayan an tashi daga barci.

15. A yi Tahajjud bayan an tashi a cikin dare domin yin hakan yana da falala mai girma. Manzon Allah (صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم) ya ce: « Mafificiyar Sallah bayan Sallar farilla, ita ce yin Sallah da dare. » *(Sahīh Muslim, shafi na 591, Hadisi na 1163)*.

Domin koyon sunnoni akan dubban batutuwa daban-daban, ku saye kuma ku karanta littatafan nan « Bahār-e-Sharī'at » Mujalladi 16, littafi mai shafi 312, da kuma « Sunnatayn aur Aadaab », littafi mai shafi 120, wanda Maktaba-tul-Madina ta tallata. Ɗay daga hanyoyi mafifita da za akoyi sunnoni itace tafiya cikin tawagar "Madani Qāfilahs" ta Dawat-e-Islami tare da masoyen Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

*Seekhnay Sunnatayn Qāfilay mayn chalo*
*Lootnay rahmatayn Qāfilay mayn chalo*



www.dawateislami.net

*Haun gi hal mushkilayn Qāfilay mayn chalo*
*Pao gey barakatayn Qāfilay mayn chalo*

*Domin koyon Sunna, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*
*Domin samun tagomashi, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*

*Domin magance matsalolinku, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs.*
*Domin samun albarka, ku yi tafiya da Madani Qāfilahs*

## Abinda ake nema a wajan Muballighīn da Muballighāt (wa'izai maza da mata)

Abinda ake nema a wajan Muballighīn da Muballighāt (Masu Wa'azi) Karanta wasu daga cikin Sunnan Annabin Rahmah, Mai Ceton Al'umma, Ma'abucin Aljannah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم a karshen duk isar da sakon yanda gorgodon iko. Kafin karanta wani abu daga Sunna, karanta sakin layi na 1 kuma a ƙarshe karanta sakin layi na 2 (Kada ƴan uwa mata musulmi su karanta sashin da ya shafi Qāfilah a sakin layi na 2).

1. Yan uwa a musulunci! a karshe, ku bari in yi anfani da wannan dama don fitar da fifikon Sunnah ta hanyar hadisai da kyawawan halaye. Manzon Allah صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم yace: « duk wanda yake son Sunnah ta, ya na so na duk wanda yake sona ya na tare ni a cikin Aljannah. » *(Mishkāt-ul-Masābīh, vol. 1, p. 55, Hadīth 175)*.

2. Domin koyon sunnoni akan dubban batutuwa daban-daban, ku saye kuma ku karanta littatafan nan « Bahār-e-Sharī'at » Mujalladi 16, littafi mai shafi 312, da kuma « Sunnatayn aur Aadaab », littafi mai shafi 120, wanda Maktaba-tul-Madina ta tallata. Ɗay daga hanyoyi mafifita da za akoyi

sunnoni itace tafiya cikin tawagar "Madani Qāfilahs" ta Dawat-e-Islami tare da masoyen Annabi صَلَّى اللّٰهُ عَلَيْهِ وَاٰلِهٖ وَسَلَّم.

### Ku ba wa wani ɗan littafin nan bayan karanta shi

Za ku sami lada ta hanyar rarraba litattafai da Maktaba-tul-Madina ta buga da littattafan da ke ɗauke da Lu'a lu'an Madina a lokacin bukukuwan aure, jana'izar, Ijtima 'aat, munasabobi, na Mīlād. Maukibi (jerin gwano), da sauransu. Yi al'adar adana 'yan littattafai a cikin kantinan ku don ba abokan cinikin ku da niyyar ribantar lada. Ku aiko da littafi ko kasida mai dauke da gyambon madani akalla guda daya ga duk wani gida da ke unguwarku tare da taimakon yara ko samarin da suka kai jarida, a kara zage damtse wajen isar da kira zuwa ga samun lada mai girma.

Babban Malamin ruhi na karni na 21, Babban masani addini Maulana Abu Bilal Muhammad Ilyas Attar Qadiri Razaviĥ دَامَتْ بَرَكَاتُهُمُ الْعَالِيَة wanda ke yaɗa karantarwar Musulunci a fiye da ɓangarori 93 na rayuwa. Idan kuna son ƙarin sani game da wanda ya assasa Dawat-e-Islami, littattafansa, ƙasidu da sassa daban-daban na Dawat-e-Islami, ku ziyarci wannan gidan yanar gizon : www.dawateislami.net.

Bugu da ƙari kuma, Dawat-e-Islami Islami tana isar da sakon Musulunci a faɗin duniya ta hanyar tashar Madani, tashar Musulunci 100% zalla. Duk inda kuke a duniya, idan kuna son kallon tashar Madani, ku bi mitoci da aka bayar masu zuwa. Idan kuna son tuntuɓar mu, da fatan za a yi mana imel a : overseas@dawateislami.net.

## Madani Channel - Paramètres de couverture globale

Transmission : Numérique

| Satellite | Type de faisceau | Position | Liaison descendante | Hz. | Polarité | Sym. Taux | FEC |
|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Asiasat (A7-C3V) | Global | 105.5 E | Bande C | 3739 | Vertical | 2815 | 3/4 |
| Intelsat 20 | Région Afrique | 68.5 E | Bande KU | 12562 | Horizontal | 26657 | 2/3 |
| Eutelsat 7 | Moyen-Orient | 7 Ouest A | Bande KU | 10815 | Horizontal | 27500 | 5/6 |
| Astra 2F | Europe | 28.5 E | Plateforme Sky | 12640 | Vertical | 22000 | 5/6 |
| Galaxy 19 | USA | 97 Ouest | Bande KU | 121835 | Horizontal | 22000 | 3/4 |

اَلْحَمْدُ لِلّٰهِ رَبِّ الْعٰلَمِيْنَ وَالصَّلٰوةُ وَالسَّلَامُ عَلٰى سَيِّدِ الْمُرْسَلِيْنَ اَمَّا بَعْدُ فَاَعُوْذُ بِاللّٰهِ مِنَ الشَّيْطٰنِ الرَّجِيْمِ بِسْمِ اللّٰهِ الرَّحْمٰنِ الرَّحِيْمِ

## DOMIN ZAMA MUSULMI MAI NAGARTA MAI RIKO DA SALLAH

Tafiyar da dukkan Daren ka a wajen Taron ljtima' Na Dawat-e-Islami , Wanda ake Gabatarwa Duk Ranar Alhamis Bayan Sallar Maghrib a Garinku ,Domin Neman Yardar Allah عزوجل Tareda kulla Niyyar koyon Sunnoni . Mayar dashi Halinka tafiya cikin tawagar Madani Qafilah kwana 3 a Duk Farkon Watan Musulumci Tareda Masoya Ma'aiki , Tareda cike Katin Madani In'amaat a kullum domin samun Fikr-e-Madinah Tareda Bayarda shi ga Wanda ya dace daga cikin 'Yan uwa Wanda Alhakin Karba yake Kansa a Garinku kwana Goman Farkon Watan Musulumci.

Manufar mu itace: 'Zamuyi kokarin sauya kawunan mu da mutanen Duniya ان شاء اللہ عزوجل Domin sauya kawunan mu , Sai Muna Amfani da Katinmu na Madani In'amaat San Nan kuma Kokarin kawo sauyi ga Mutanen Duniya Sai Muna shiga cikin Tawagar Matafiya Madani Qafilahs ان شاء اللہ عزوجل

MADANI CHANNEL

DAWAT-E-ISLAMI

Aalami Madani Markaz, Faizan-e-Madinah, Mahallah Saudagaran
Purani Sabzi Mandi, Bab-ul-Madinah, Karachi, Pakistan.
UAN: +92 21 111 25 26 92 I Ext: 1262
Web: www.dawateislami.net I E-mail: translation@dawateislami.net